## ABOUT CITAD

CITAD (www.citad.org)
Is A Capacity Building Civil Society Organization Whose Activities Covers Research, Advocacy, Training And Publicity In All Areas Of Icts.
Its Vision Is; A Knowledge-based Democratic Society Free Of Hunger While Its Mission Is; Using ICTs To Empower Citizens For A Just And Knowledge-based Society That Is Anchored On Sustainable And Balanced Development.

**MAIN OFFICE:**
3rd Floor, NISTF Building, No.1A, Social Insurance Road, Behind Trade Fair Complex, Zaria Road, Kano. P.O. Box 10210, Kano, Nigeria.
GSM: 0800-68078282, 080-54362931, 070-33427467 •
E-mail: info@citad.org, Citadev@gmail.com, citad4peace@citad.org,
Website: www.citad.org, www.citad4peace.org.ng

**BAUCHI OFFICE:**
NUJ Secretariat, Opposite Reinsurance House, Ahmadu Bello Way, Bauchi State.
GSM: 08064867312

**CITAD**.....*A Knowledge-Based Democratic Society Free of Hunger*

*Tsarawar*
Cibiyar Bunƙasa Fasahar Sadarwa Da Ci Gaban Al'umma (CITAD)
Tare Da
Gudummawar Ƙungiyar ActionAid Ta Najeriya (AAN)

# KUNDIN SAMAR DA CIGABAN GARIN GAMOJI



CENTRE FOR INFORMATION TECHNOLOGY AND DEVELOPMENT

# KUNDIN SAMAR DA TSARIN CI GABAN GARIN GAMOJI

*Tsarawar*

**Cibiyar Bunƙasa Fasahar Sadarwa Da Ci Gaban Al'umma (CITAD)**
**Tare Da**
**Gudummawar Ƙungiyar ActionAid Ta Najeriya (AAN)**





## ABUBUWAN DA KE CIKI


Shafin Farko....i
Jadawali....ii
Godiya....1
Gabatarwa....2
Manufa....3
Hanyoyin Da Aka Yi Amfani Da Su....3
Tsarin Da Aka Yi Amfani Da Shi....3/4
Cikakken Bayani Game Da Garin Gamoji....4/6
Tarihin Garin Gamoji....6
Taswirar Garin Gamoji....7/8
Yanayin Zamantakewa....8/9
Lafiya....9
Ilimi....9/11
Juyawar Yanayin....11/13
Jadawali Ayyukan Mazan Garin Gamoji Na Yau da Kullun....13/14
Jadawali Ayyukan Matan Garin Gamoji Na Na Yau Da Kullun....15
Jadawali Ayyukan Yaran Garin Gamoji Na Yau Da Kullun....16
Kadarori....17
Tantance Matsalolin Da Ke Addabar Garin Gamoji....17/18
Tantance Haƙƙoƙin Mata....21
Take Haƙƙoƙin Ɗan Adam....22/23
Kalubalen Da Ke Fuskantar Garin Gamoji A Halin Yanzu....23/27
Tantance Matsaloli Ta Amfani Da Bishiyar Matsaloli....27/28
Kungiyoyi/Hukumomi da Masu iko da Zasu iya Tallafawa Gamoji....29/30
Tantance Yanayin Karfin iko (Nazari Kan Waɗanda Keda iko)....30/31
Tantance Matsalolin Da Ke Addabar Garin Gamoji....32
Tantance Hanyoyin Samun Bayanai....32/33
Tsarin Da Aka Shirya Gudanarwa Na Al`Umar Garin Gamoji....33/34

# GODIYA

Wallafawar wannan littafi yasamu yiwuwane tareda tallafi daga Sashin Kula da Cigaba na ƙasa da ƙasa na Gwamnatin Birtaniyya (DFID ta hannun ƙungiyar ActionAid Nigeria (AAN). Dole ne a yabawa wannan Cibiya ta ActionAid saboda jajircewa ta wajen Bunƙasa Demokuraɗiyya ta hanyar wayar da Jama'a su fahimci Demokuraɗiya.

Muna godiya ta musamman ga Shugaban Cibiyar Fasahar Sadarwa da Ci gaban Al'umma (CITAD), Y.Z. Ya'u domin kasancewarsa jigo wanda ya bada gudummawa ga kammaluwar wannan Littafi.

Godiyar mu bazata cikaba sai mun yaba da Kyakkyawar fahimta da hadin kai da ma'aikatan CITAD. Haka kuma mun yabawa da ƙoƙari da himmar Malam Ahmad AbdullahiYakasai, da Isyaku Garba' da Abubakar Auyo da Mukhtar Sulaiman Umar da Abdullahi Jido da Harira Abdulrahman wanda suka hana kansu hutu domin tabbatar da kammaluwar wannan Kundi.

Muna miƙa cikakkiyar godiyarmu ga 'Yan kwamitin aiwatar da kundin wannan Gari na Gamoji da Mai Gari da Dagaci da kuma dukkannin waɗan da suka tallafa wajen gudanar da tsarin shirin wannan kundi, babu shakka zai ingan ta shirin nan gaba.





# GABATARWA

Wannan kundi na cigaban wannan gari yana ɗauke da gabaɗayan bayanai filla-filla da kuma taƙaitattun abubuwan da suka shafi garin Gamoji da ke ƙaramar hukumar Gaya a jihar Kano a tarayyar Najeriya. Wannan kundi zai zama wani hujjane wajen tabbatar da gaskiyar al'amura ga jama'ar garin Gamoji. Kundin, ya yi cikakken bayanin garin da mutanensa da kuma albarkatun ƙasa da Allah Ya huwace masa. An tattaro waɗannan bayanai ne daga wajen wasu keɓantattun mutane mazauna garin ta hanyar yin amfani da tsarin waiwaye adon tafiya domin yin bitar abubuwan da suka gudana da kuma tsarin nan na CITAD da ActionAid wanda ke bai wa kowa damar bayar da gudummawa don faɗakar da mutane sanin muhimmancin kowa ya shiga a dama da shi a al'amuran zaɓe wanda aka fi sani da (SCEEP).

Tsarin zai zama wani ginshiƙi na aiki tare da wasu garuruwan a ƙoƙarin saita al'umma kan gwadaben da za su rinƙa bibiyar abubuwan da gwamnatoci da wakilansu ke gudanarwa. Haka kuma, wannan kundin zai samar da wata kafa ta yin aiki tare tsakanin al'ummar garin da waɗanda suka zaɓa zuwa matakai daban-daban. An samar da kundin ne ta bin managartan tsare-tsare da wannan ƙungiya ta yi a baya, aka tattaro ƙwararru suka yi aiki ƙarƙashin inuwa ɗaya.

Hanyar amfani da tsarin waiwaye adon tafiya na yin amfani da cikakken bincike kamar binciko dangantakar mahukunta da haƙƙoƙin al'umma musamman mata da gano abubuwan da ke yi wa garin barazana da binciko ƙungiyoyi da mutanen da za su iya tallafawa da fahimtar hanyoyin sadarwa da al'ummar garin ke amfani da su da kuma matsalolin da suke ci musu tuwo a ƙwarya.
Domin cimma nasara abubuwan da aka ambata a sama, ActionAid ta aiwatar da tsarin waiwaye adon tafiya a garin, ta amfani da sassa bakwai na tsarin tantancewar bayanan da aka tattara domin su zama ginshiƙai na ƙarfafa gwiwa wanda zai ciyar da garin gaba yadda ake buƙata.

## MANUFA

Manyan manufofin wannan kundi su ne kamar haka:

- Gano tare da adana al'amuran da suka shafi garin Gamoji tare da fitar da wani tsari na shigo da al'ummar yankin don yin aiki tare.
- Zaburar da al'umma wajen neman abubuwan cigaban garin daga wakilansu a ɓangarori daban-daban.
- Tallata ƙwarewa da ilimi da kuma abubuwa da garin Gamoji ke fatan samu a dunƙule domin samun sauƙin bibiya.

## HANYOYIN DA AKA YI AMFANI DA SU

Hanyoyin da aka bi wajen aiwatar da aikin sun haɗa da:

- Tattaunawa tun a karon fari tsakanin dattawan garin Gamoji da CITAD.
- Ziyarce-Ziyarce: An ziyarci wurare daban-daban tare da ganawa da mutanen garina tsawon kwanaki domin samun cikakkun bayanai na ɓangarorin nan bakwai na Reflection Action.
- Taron tantancewa da rubuta rahoton abubuwan da aka gano.

## TSARIN DA AKA YI AMFANI DA SHI

An yi amfani da abubuwa daban-daban wajen tantance ɓangarori nanbakwai na waiwaye adon tafiya wato Reflection Action.

An yi amfani da taswira wajen binciko matsalolin da ke addabar garin.

An yi amfani da jerin gwanon haƙƙoƙi ɗan Adam wajen gano haƙƙoƙin al'ummar garin Gamoji.

Jera abubuwa mafi sauƙi ya taimaka wajen tsara al'amuran da suka fi muhimmanci bi da bi waɗanda al'ummar garin suka gano.





An yi amfani da bishiyar-matsaloli domin fahimtar abubuwan da suka haddasa matsalolin da tasirinsu da kuma tattaunawa mai zurfi a kansu.

An yi amfani da salon tantance cibiyoyi da mutanen da za su iyabayar da tallafi domin gano waɗanda za su iya hoɓɓasa kuma suke da ikon kawo canji ga abubuwan da garin ke buƙata.

An yi amfani da tsarin zane naVenn domin a tantance matakin tasirin da cibiyoyi da mutanen da za su iya taimakawa da alaƙarsu da garin.

An yi amfani da salon yanar-gizo wajen tantance haƙƙin mata.

Tsarin tantance matsaloli ya fitar da abubuwa daban-daban da ka iya cutar da garin.

Zanen hanyoyin sadarwa ya tantance hanyoyin da al'ummar garin ke isar da saƙonni tsakaninsu da sauran garuruwa da waɗanda za su iya bayar da gudummawa. A ƙoƙarin aiwatar da tantance abubuwa daban-daban, an tattauna da kowa da kowa, an tattauna a ƙungiyance don a yi tambayoyi da kuma yin bincike mai zurfi domin a samu tantancewa mai inganci.

## Cikakken Bayani Game Da Garin Gamoji

| | |
|---|---|
| Sunan Garin: | Gamoji |
| Karamar Hukuma: | Gaya |
| Jiha: | Kano |
| Adadin Al'umma: | 20,000 (Maza: 8, 250 Mata: 11750) |

Ajujuwan Shekarun Al'ummar Garin

| | |
|---|---|
| Shekara 0 zuwa 5: | 5000 |
| Shekara 6 zuwa 10: | 4000 |
| Shekara 11 zuwa 18: | 3000 |
| Shekara 19 zuwa 30: | 3000 |
| Shekara 31 zuwa 40: | 2500 |
| Shekara 41 zuwa 50: | 1000 |

Shekara 51 zuwa 60: 750
Shekara 61 zuwa 70: 500
Shekara 70 zuwa sama: 250
Sana'oi /Aikin yi: Noma da Kananan 'Yan Kasuwa
Kiwo: Shanu, Awaki da Tumaki

Kuɗaɗen da ke shigowa/Kuɗaɗen da ake kashewa
Matsakaicin abin da ke shigowa mutum a shekara: **N200, 000**
Matsakaicin abin da mutum yake kashewa a shekara: **N200, 000**
Matsakaicin abin da ma'aikaci yake samu a shekara: **N300,000**
Matsakaicin abin da ma'aikaci yake kashewa a shekara:**N400, 00**

Lafiya

Ɗakin Shan Maganin Garin:Kilomita2.25Km negwargwadon nisanƊakin Shan Maganin da al'umma. Wannan shi yake daidai da 2.25 KM/hour a ma'aunin lokaci da kilomita. Ɗakin Shan Maganin nada ma'aikatan lafiya guda 5, maza 4 mace 1 duk da yake dai ba kasafai ake samunsu gabaɗaya a asibitin ba. Idan kuma aka sami ɓarkewar cututtuka sukan sanar da hukumar da abin ya shafa ta hannun Dagacin garin dasauran jami'an lafiyar. Waɗanda cututtuka suka fi yiwa barazana su ne ƙananan yara yan ƙasa da shekaru 5.Mutanen wannan gari sun bayyana cewa matakan haihu a gida a mafi yawan lokaci wani lokacin kuma wasu matan tsiraru kan haihu a ɗakunan shan maganin garin. Idan haihuwa tazo da tangarɗa akan kai mata asibitin Gaya su haihu a can. Kodayake dai anfi haihuwa a gida tare da taimakon ungozomomin gargajiyar garin. Babu wani cigaba da aka samu a shekaru 3 baya ta harkokin da suka shafi lafiya a garin.

Ilimi

Makarantu: Makarantar firamaren garin nada nisan 2.25 km/hour daga garin, guri guda makarantar take da Ɗakin Shan Maganin garin.





IILIMI

Makarantu: Akwai makarantun firamare 2 da ƙaramar sakandare 1.

| | | | |
|---|---|---|---|
| Adadin yaran da suka shiga makaranta a halin yanzu: **1,289** | Adadin yara maza: 893 | Adadin yara mata: 396 | Adadin 'yan ƙasa da shekara 5: 188 |
| | Adadin yara 'yan shekaru 6 zuwa 10: 389 | Adadin 'yan shekaru 11 zuwa 15: 421 | Adadin 'yan shekaru 16 zuwa 20: 291 (idan ana buƙata) |
| Adadin waɗanda suka kammala firamare a garin:**666** | | | Adadin Maza:**610** |
| | | | Adadin Mata: 56 |
| Adadin waɗanda suka kammala sakandare a garin: 41 | | | Adadin Maza: 31 |
| | | | Adadin Mata: 10 |
| Adadin waɗanda suka kammala makarantar gaba da sakandare a garin: **125** | | | Adadin Maza: 120 |
| | | | Adadin Mata: 5 |
| Adadin waɗanda ba su taɓa zuwa makaranta ba a garin: **19,000** | | | Adadin Maza: **9,000** |
| | | | Adadin Mata: 10,000 |

Masu Buƙata Ta Musamman (PWDs): 18



## TARIHIN GARIN GAMOJI

Gamoji ƙauye ne da ayyukan noma suka fi shahara ga al'ummar garin.Al'ummar garin hausawa ne da Fulani.Hausa shi ne yaren da aka fi yi a ko ina a wannan gari. Tun da can, al'ummar garin Gamoji sun riƙi nomada kiwo a matsayin Hanyoyin samun kuɗin shiga. Sauran hanyoyin samun kuɗaɗen shigar mutanen wannan gari sun haɗa da ƙira, rini, saƙa, da kuma ginin tukwane.Allah ya albarkaci wannan gari da yawan mutane da albarkatun tsirrai daban-daban. Garin yanada rijiyoyi da dama wanda suka haɗa da na tuƙa-tuƙa ga kuma ƙasar noma. Gamoji nada makarantun firmare guda 3, babbar makarantar firamaren garin nada nisan 2.25km daga kauyukan wajengarin. Adadin al'ummar garin sun kai 20,000 haka kuma garin ya haɗa ƙananan ƙauyuka kimanin 36.

## TASWIRAR GARIN GAMOJI

Zanen taswirar ya soma ne da tattaunawa mai zurfi don sanin albarkatun ƙasar da Allah ya horewa garin da kuma matsalolin dake addabar garin. A yayin wannan ƙoƙari, an gano albarkatun ƙasar da Allah ya horewa garin da ababan more rayuwa da sauran ni'imomin da Allah ya huwace musu. Albarkatun ƙasar da garin ke da shi sun haɗa da tsirrai, koguna kamar kogin Dudduru da ƙasar nomada burtalan kiwo.





Figure 1: Taswirar Garin Gamoji







Figure 2: Mata da suka halarci zaman tsara Kundin



### YANAYIN ZAMANTAKEWA

Garin Gamoji na cikin ƙaramar hukumar Gaya, gari ne dake da kimanin nisan ..KM daga garin Kano, garin na da yawan al'ummar da yakai sama da 20, 000 (8,250 maza da 11,750mata). Babu wata ƙididdiga da ta nuna yanayin jagoranci a tsakanin iyalai a wannan gari. Yara dake tsakanin shekaru 0 zuwa 5 su suka fi yawa a wannan garin, duba ajujuwan shekarun al'ummar garin domin ƙarin bayani.

Bugu da ƙari, yawancin al'ummar Gamoji manoma ne da ƙananan yan kasuwa. Manoman na noman Kayan abinci kamar su Gero, Dawa da Rogo da Kayan Miya da N 200, 000 a matsayin matsakaicin kuɗin shiga a shekara ga magidanci. Da kuma N200,000a matsayin matsakaicin kuɗin kashewa a kullun ga magidanci.

Yawan mazauna garin kan kashe yawancin kuɗaɗen da suke samu a kullun saboda noman kayan miyar da suke yi. Akwai tsirarun ma'aikatan gwamnati a garin wanda suke samun N 300, 000da N500,00 a matsayin matsakaicin kuɗaɗen shiga da batarwa a shekara da.




**LAFIYA**

Al'ummar garin na amfani da wani ɗan ƙaramin ɗaki dake jikin makarantar firamaren garin a matsayin ɗakin shan magani.Ɗakin yayi matuƙar kaɗan idan an kwatanta da abubuwan da suka shafi lafiyar jama'ar garin. Hakan yayi dai-dai da ƙarancin ƙwararrun ma'aikatan lafiyar da ake da fama dashi dana magani da rashin kayayyakin kula da lafiya da kuma rashin ɗakin karbar marasa lafiya da sauransu, wannan shi yasa ake kai marasa lafiya babban asibitin garin Gaya wanda yake da nisa daga garin. Haka kuma wannan ya jawo yawaitar samun mutuwar mata masu juna biyu da saurin yaɗuwar cututtuka da kuma ɓari ga mata masu juna biyu. Don haka, yana da mutuƙar muhimmanci ga gwamnati ta samar da ɗakin shan magani babba na zamani tareda isassun kayayyakin aiki da kuma ƙwararrun ma'aikata domin inganta rayuwar al'ummar garin.



ILIMI

Garin Gamojina da makarantun firamare guda 3 waɗanda suke ciki da kauyukan garin. Sai dai yawancin ajujuwan basu da kujeru da teburan zama, wanda ake dasu kuma sun lalace. Su kansu ajujuwanma suna buƙatar Gyara domin samun ingantaccen koyo da koyarwa ga malamai da ɗaliban makarantar. Makarantar sikandire ɗaya ce a garin. Sikandiren na zaman wucin gadi ne a ɗaya daga cikin firamaren garin. Hakan na nufin cewa ita kanta sikandiren kyautuwa yayi ta koma matsuguninta na dundundun. Akwai makarantar islamiyya ɗaya a garin, kodayake ita kanta makarantar islamiyyar batada





isassun ajujuwan da zasu iya ɗaukan ɗaukacin ɗalibanta. A lokaci guda kuma ga buƙatar da ke akwai na malaman islamiyya.A garin na Gamoji, 1,289 ne adadin yaran da suka shiga makaranta a halin yanzu, 893 daga cikinsu maza ne yayinda 396 mata ne. wannan shi yake nuna cewa adadin mazan da suke karatun boko ya ɗara na mata. Haka kuma wannan na nuna cewa akwai buƙatar saka yara mata a makarantu a garin domin su cimma yawan yan uwansu maza.

Akwai adadin mutane 666 waɗanda suka kammala firamare a garin, 610 daga cikinsu maza yayinda 56 mata ne. Haka kuma adadin waɗanda suka kamala sikandire a garin a halin yanzu shi ne mutum 41, 31 daga cikinsu maza yayinda 10 daga cikinsu mata ne. Bugu da ƙari, adadin mutane 125 ne suka kammala makarantun gaba da sikandire a garin, 120 daga ciki maza sauran 5 ɗin kuma mata ne. wannan shi yake nuna cewa ƙalilan daga cikin matan garin ake bari zuwa makarantun gaba da sikandire idan an kwatanta da yan uwansu maza. Sannan kuma akwai adadin mutane 19,000 waɗanda basu taɓa zuwa makaranta ba (9,000 mata 10,000 mata).

Akwai buƙatar dake akwai na ganin gwamnati ta katange makarantun garin, ganin yadda samari ke shiga makaratun a kodayaushe su gabatar da munanan ɗabi'u kamar shaye-shayen taba da miyagun ƙwayoyi wanda aka gaza shawo kai. Duba da yanayin, makarantun suna bukatar da a daddasa bishiyu ciki da kewaye do ingan ta wajen koyo da kyakkyawan yanayi.

Anyi amfani da Shirin bunƙasa damar samun ilimi PRS domin tantance inganci ilimi a garin Gamoji.Shirin bunƙasa damar samun ilimi PRS ya fayyace haƙƙoƙi guda 10 da aka samu daga dokokin ƙasa misali anyi amfani da kundin tsarin mulkin ƙasa da tarukan kare Haƙin Dan Adam wajen tantance ingancin ilimi a garin na Gamoji. Babbar manifar wannan shiri na PRS shi ne shigar da yan ƙasa cikin tsarin bunƙasa ilimi. Anyi amfani da kundin wajen tantance mizanin fahimtar damar samun ilimi musamman ta fuskar al`umar wannan yankin su san cewar damar

su ce. Tare da mizani mai lamba 1 mafi ƙaranci da lamba 5 mafi girma.Jadawalin da ke tafe yayi ƙarin haske.

## GA JEREN HAKKOKIN:

| LAMBA | HAKKOKI (SHIRIN BUNKASA DAMAR SAMUN ILIMI PRS NA GARIN GAMOJI) | TANTACEWA (1 MAFI KARANCI, 5 MAFI GIRMA) |
|---|---|---|
| 1. | Haƙƙoƙin samun kyakkyawan ilimi kuma kyauta | 1 |
| 2. | Haƙƙoƙin rashin nuna wariya | 3 |
| 3. | Haƙƙoƙin samar da isassun kayayyakin more rayuwa | 4 |
| 4. | Haƙƙoƙin samara da ƙwararrun malamai | 4 |
| 5. | Haƙƙoƙin samar da wajen zama mara haɗari | 5 |
| 6. | Haƙƙoƙin samar da tsarin koyarwar da ya dace (manhaja) | 1 |
| 7. | Haƙƙoƙin sanin 'yancin kai | 2 |
| 8. | Haƙƙoƙin a dama da mutum a wajen ɗaukar mataki | 1 |
| 9. | Haƙƙoƙin samar da makarantu ingantattu marasa ƙunbiya-ƙunbiya | 1 |
| 10. | Haƙƙoƙin samar da ingantacciyar koyarwa | 5 |




## JUYAWAR YANAYIN

Garin Gamojinada yanayi iri biyu, rani da damina.Ana samun yanayin rani ne daga watan Nuwamba zuwa watan Afrilu.Damina kuwa tana farawa daga watan Mayu, inda ruwa yakan kankama tsakanin Agusta da Satumba. Jihar Kano kacokan ta fi samun yanayin zafi da yawa, ruwan sama(watau damina) yawanci akan same shi ne a watannin Mayu da Yuni da Yuli da Agusta da kuma Satumba. Kano na samun rani a watannin Janairu da Fabrairu da Maris. Akan samu matsakaicin zafi a watan Afrilu, yayin da sanyi ya fi tsananta a watan Nuwamba. Satumba shi ne ne watan da aka fi samun ruwan sama, haka kuma Janairu ne watan da rani ya fi tsamari. Ayyukan noma a garintsaka-tsaki ne saidai ƙananan kasuwanci.Jama'ar garin Gamoji kan shirya domin ayyukan noma tsakanin watan Maris da Afrilu. Jadawalin da ke biye yana nuna yadda yanayin ya karkasu da kuma yadda ayyukan suke gudana a tsakanin waɗannan lokutan.





Figure 3: Yanayin Garin Gamoji A Tsawon Shekara




Karin haske: HSama da Gaske M Matsakaici L Kasa Sosai



Figure 4: Yanayin Garin Gamoji A Tsawon Shekara

Tsakanin watan Fabrairu da watan Afirilu ake gyaran gona a garin Gamoji domin shuka. A lokutan shukar kuma akan shuka Gero, Dawa, Masara, Gyaɗa,Tattasai da Wake. Ana danganta wannan lokacin da rashin kuɗaɗen shiga saboda ayyukan noma da kuma rashin kyawun yanayi na sadarwa saboda katsewar hanyoyin sadarwa da kuma katsewar hanyoyin sufuri zuwa maƙotan gararuwa.

## JADAWALI AYYUKAN MAZAN GARIN GAMOJI NA YAU DA KULLUN

| LOKACI | AYYUKA |
|---|---|
| 5:00 zuwa 7:00 na safe | Lokacin Sallah, gaida iyaye da dattijai, saurarar rediyo da kuma karin kummalon safe. |
| 7:00 na safe zuwa 1:30 na rana | Zuwa gona, zuwa makaranta, ofis da guraren aiki, kasuwanci, ziyartar iyalai da kallon wasan ƙwallon ƙafa. |
| 1:30 na rana zuwa 4:00 na yamma | Sallah, zuwa makarantun islamiyya, baccin rana, cin abincin rana, kallon wasan ƙwallo da kuma ɗaukan talla. |
| 4:00 zuwa 6:00 na yamma | Sallah, wasan ƙwallon ƙafa, zuwa makarantun islamiyya, yammaci a gona da kuma ɗebo ruwa. |
| 6:00 na yamma zuwa 10:00 na dare | Sallah, hira, zuwa neman aure, zuwa gidajen kallo da kallon wasan ƙwallon ƙafa. |
| 10:00 na dare zuwa 12:00 na dare | Dandalin sada zumunta, sallolin dare, zirga-zirga domin tsaro da bacci. |









**Figure 5: Men's Daily Activities**

# **Figure 5:** JADAWALI AYYUKAN MATAN GARIN GAMOJI

| LOKACI | AYYUKA |
|---|---|
| 5:00 zuwa 6:00 na safe | Sallah, saurarar rediyo. |
| 6:00 zuwa 9:00 na safe | Shirya karin kumallo, shirya yara zuwa makaranta, wanke-wanke da sharar gida, wasu matan kuma su gudanar da sana'o'insu na safe. |
| 9:00 zuwa 11:00 na safe | Wanke kayan sawa da gyaran gida. |
| 11:00 na safe zuwa 2:00 na rana | Shirya abincin rana, wasu matan kuma su gudanar da sana'o'insu na rana. |
| 2:00 na rana zuwa 4:30 na yamma | Wanka, ziyarar yan uwa da abokan arziƙi da yin sallar la'asar. |
| 4:30 na yamma zuwa 8:00 na dare | Shirya abincin dare, yin sallar magriba da saurarar labarai. |
| 8:00 zuwa 1:00 na dare. | Tattaunawa tsakanin iyalai da tafiya domin kwanciyar bacci. |





**Figure 6: Jadawali Ayyukan Matan Garin Gamoji**





# JADAWALI AYYUKAN YARAN GARIN GAMOJI NA YAU DA KULLUN

| LOKACI | AYYUKA |
|---|---|
| 6:00 zuwa 8:00 na safe | Lokacin sallah, halartar makaratun allo, Karin |
| 8:00 na safe zuwa 1:00 na rana | kummalon safe, gaida iyaye da dattijai, talla da yin wanka. Zuwa makaranta, noma, kiwo, yin ciyawa da zuwa talla. |
| 1:00 na rana zuwa 4:00 na yamma | Sallar azhar, bacci, sallar la'asar, cin abincin rana da zuwa talla. |
| 4:00 na yamma zuwa 7:00 na dare | Wasanni, zuwa makarantun islamiyya, nomada talla. Sallolin dare, zuwa makarantun allo, wasanni, talla, |
| 7:00 zuwa 10:00 na dare. | kallon wasan ƙwallon kafa, halartar tarukan addini da zuwa kwanciyar bacci. |





**Figure 7: Jadawali Ayyukan Yaran Garin Gamoji**




KADARORI

Adadin waɗanda suka mallaki gonaki ko suke gudanar da ƙananan san'o'i a garin na Gamoji maza da mata shi ne 251 (Maza 210 mata 41, kamar yadda ɗaya daga cikin mambobin samar da kundin ya zayyana). Wannan shi ya nuna cewa maza sunfi gudanar da noma ko ƙananan sana'o'i akanmatan garin. Haka kuma wannan na nufin sai anyi ƙoƙari da gaske domin ganin adadin mata ya ƙaru ta yadda za a bunƙasa harkokin rayuwarsu. A wani gefen kuma, za a iya bunƙasa tattalin arziƙin matan garin wajen samar musu da sana'o'i kamar noma da kiwo.



TANTANCE MATSALOLIN DA KE ADDABAR GARIN GAMOJI

Al'ummar wannan garin su bayyana matsaloli guda 3 dake damunsu. Matsalolin su ne: Matsalar zaizayar ƙasa, ambaliyar ruwa, matsalar katsewar hanyoyin sadarwa da mutuwar mata masu juna biyu.

Zaizayar Kasa: Garin Gamojina samun mamakon ruwan sama tsakanin watan Yuli da Agusta. Ruwan saman kan zo da matsalar anbaliya saboda yawansa. Wannan yanayin kan ɓata wasu sassan hanyoyin mota da na mutane, haka kuma yakan ɓata gonaki dama amfanin gona.

Kakkatsewar Hanyoyin Sadarwa: wannan gari na fama da matsalar ƙaranci hanyoyin sadarwa da gadoji tsakanin kogunan da suka raba garin gida biyu. Duk lokacin da akayi ruwan sama ayyukan kasuwanci kan tsaya cak na wasu awanni ko yini guda saboda mutane baza su iya tsallaka kogunan ba. Hakan kan jawo katsewar al'ammura da zuwan yara makaranta, yayinda yara kan tsunduma farauta a dazuzzuka a irin waɗannan lokutan. Wannan shi yake jawo dagulewar harkokin kasuwanci da dagulewar karantun yara yanda yara kan tsunduma wasu miyagun halaye kamar shaye-shaye da sauran miyagun ɗabi'u.





Mutuwar Mata Masu Juna Biyu: Jinkirin da akan samu na naƙuda yayin haihuwa kanyi barazana ga rayuwar mata masu juna biyu. A wasu lokutan, matan kanyi fama da wahalhalu a gida ko akan hanyar zuwa asibiti saboda jinkirin da akan samu kafin a isa asibiti saboda rashin gadojin da kyawawan hanyoyin mota da za a iya tsallaka kogi. Wannan na faruwa ne a lokutan damuna kuma yakan jawo asarar rayuka.

Jadawalin dake tafe hanya ce ta jeran matsalolin dake addabar wannan gari.

| MASALA | YIYUWAR FARUWAR MATSALA | | | TASIRIN MATSALAR | MA'AUNI | | | MATAKIN DA AKA ƊAUKA NA RAGE FARUWAR MATSALAR |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| | H | M | L | | H | M | L | |
| Karuwar mutuwar mata masu juna biyu yayin haihuwa | | ✓ | | Tsaiko saboda ƙarancin kyawawan hanyoyi da gadoji | | ✓ | | Akwai buƙatar gwamnati ta samar da ƙarin ɗakunan shan magani da samar da ƙarin jami'an lafiya da kayayyakin aiki ƙarin akan na da. |
| Katsewar Hanyoyin Sadarwa | | ✓ | | Taɓarɓarewar kasuwanci | | ✓ | | Akwai buƙatar kamfanonin sadarwa su bunƙasa ayyukan su a yankin sannan kuma a gina gadoji a ɗaukacin hanyiyin da suka ratsa ta cikin kogi. |
| Ambaliyar ruwan Kogi a lokacin damuna | ✓ | | | Tana hana yara zuwa makaranta Tana hana Aal'umma zuwa Asibiti da kuma katsewar kasuwanci da sadarwa | ✓ | | | Garin bashi madatsun ruwa da magudanan ruwa, akwai buƙatar gwamnati ta samar da magudanan ruwa da Dam wanda zasu rage matsalar ambaliyar ruwa a garin |




TANTANCE HAKKOKIN MATA‘

'Yancin mata shi ne Haƙƙoƙinda aka keɓe musamman domin mata da 'yanmata a ƙasashen duniya masu yawa. A wasu wuraren, ire-iren waɗannan Haƙƙoƙinana tabbatar da su ne ta hanyar yi musu doka da tsarin zamantakewar al'umma. A wasu wuraren kuwa, a iya cewa an yi watsi da su. Lamuran da ake dangantawa da haƙƙin mata ba a takaita su ga 'yancin yin zaɓe ko takaita haihuwa kaɗai ba. Ya haɗa harda yancin shiga a dama da su a zaɓe, riƙe ofisoshin gwamnati, kare su daga yi musu fyaɗe, damar ɗaukan albashi na bai ɗaya, mallakar kadarori, samun ilimi ingantacce, yin aikin soja, yin kwangiloli da damar auratayya ko kuma zama iyaye.

An sami cigaba dangane da haƙƙoƙin mata a shekarau da yawa a wannan gari. Mata da yan mata ana basu damar su gaji filaye daga mazajensu ko iyayensu da suka rasu haka suna da damar sayan filayen idan buƙatar haka ta tashi. Ana basu damar mallakar fili domin noma kuma sunada iko akan abubuwan da suka noma.

Garin Gamoji ya ƙunshi ƙananan ƙauyuka da dama. Sai dai mata a wannan gari basa shiga a dama dasu wajen sha'anin mulki da zartarwa.

A garin Gamoji mata na gudunar da yan sana'o'insu da kasuwancinsu. Kuma suna iko akan kuɗaɗen da suka samu a waɗannan kasuwancin. Suna amfani da Kuɗaɗen da suka tara ta hanyar sana'o'insu domin biyan buƙatunsu na yau da kullum harma kula da harkokin gida. Da yawansu suna kiwon dabbobi kamar Shanu, da Tumaki da tsuntsayen gida.

Anyi amfani da ma'aunin cobweb domin tantance haƙƙoƙin mata. Amfani da wannan ma'aunin zai sa a fahimci abubuwan da suke kawo mu cikas wajen cigaban su da kuma matsayinsu a cikin al'umma.



KUNDIN SAMAR DA TSARIN CIGABAN GARIN GAMOJI 2016





Figure 8: Ma'aunin Cobweb na Tantance Haƙƙoƙin Mata a Garin Gamoji





**Figure 9: Ma'aunin Cobweb na Tantance Haƙƙoƙin Maza a Garin Gamoji**

| ƁANGARE | SAKAMAKO (MATA) | SAKAMAKO (MAZA) |
|---|---|---|
| Damar samun ayyukan yi | 1 | 2 |
| Shugabanci | 1 | 1 |
| Kuɗin Shiga | 2 | 1 |
| Kula da gida | 2 | 1 |
| Mallakar Kadarori | 3 | 2 |
| Tsaro | 5 | 5 |
| Samun damar ilimi | 2 | 2 |
| Zartar da hukunci kan al'amuran al'umma | 1 | 1 |
| Damar sarrafa albarkatu | 4 | 5 |
| Shiga al'amuran al'umma | 1 | 1 |

DOMIN TABBATAR DA WANNAN JADAWALI

Jadawalin na sama na nuna tazarar da ke tsakanin maza da mata a lokacin aikin tantance haƙƙoƙin mata. Abin sha'awa, akwai daidaito na kurkusa a ratar da aka samu a tsakaninsu, wanda yake nuna cewa al'ummar garin sun fahimci banbancin da ke tsakanin maza da mata.

A garin Gamoji mata basu da ta cewa a harkar shugabanci, sannan shiga a dama dasu sha'anin al'amuran al'umma bai taka kara ya karya ba. Duk da irin ƙoƙarinsu ba a saka su wajen zartar da hukunci. Sukan shiga a dama dasu a al'amuran kasuwanci (ƙananan sana'o'i) amma banda harkar shugabanci.



Matan Garin A Wajen Tantance Haƙƙoƙin Mata







Matan Garin A Wajen Tantance Haƙƙoƙin Maza




**TAKE** HAKKOKIN ƊAN **ADAM**

Duba da rijistar haƙƙin Ɗan Adam, an gano cewa an takewa mutanen garin Gamoji waɗannan haƙƙoƙin:

Haƙƙin ingantacciyar lafiya
Haƙƙin Samun Ilimi
Haƙƙin Samun Abubuwan more Rayuwa
Haƙƙin Samun ingantaccen Ruwan Shada wutar lantarki

Waɗannan haƙƙoƙi nada alaƙa da matsalolin da suke damun wannan garin.Dangane da wadannan matsalolin da ake takewa, al'ummar wannan garin sun yanke cewa matsalar ingantacciyar hanya da gadoji(sune manyan matsalolin da aka tauye musu kuma matsalolin sune ummul aba isin rashin cigaban wannan yanki.Mutanen wannan garin basu samun ingantaccen ilimi da lafiya a sauƙaƙe musamman lokacin damuna). Daɗin daɗawa kuma an tauye musu haƙƙin ingantacciyar lafiya saboda ƙarancin asibiti da ƙarancin ma'aikatan lafiya a ɗakunan shan maganin garin.

| Jihar /LRP | KANO | | | KARAMAR HUKUMA | GAYA | | GARI | | KADEMI | |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| Rashin cancanta/ cancanta a samu (mata, yara, talakan da ba shi da fili ko rukunin jama'ar da aka gano) | Adadin waɗanda suka cancanci su samu a yankin da aka yi shirin | | Al'amari | Abubuwan da suka haddasa | Haƙƙoƙin da aka tauye | Kundin tsarin mulki | Adadin waɗanda suka cancanci su samu damar da suke neman haƙƙinsu a farkon fara shirin | | Waɗanda nauyin yin aikin ya hau kansu | Sauran muhimman masu ruwa da tsaki |
| | Namiji | Mata | | | | | Namiji | Mata | | |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 8,250 | 11,750 | Ilimi | - Rashin Kyakkyawar Hanya<br>- Rashin Ingantaccen Shugabanci<br>- Rashin Kyakkyawar Hanya | Haƙƙin ingantaccen Ilimi | Kundin tsarin mulki | 8,250 | 11,750 | - Ma'aikatar Ilimi<br>- Ma'aikatar Ilimi Ta bai ɗaya (SUBEB) | Kwamitin Iyayen Yara(PTA)<br>Kwamitin SBMC |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 8,250 | 11,750 | Lafiya | Rashin ingantaccen shugabanci | Haƙƙin samun ingantattun kayayyakin kula da lafiya | Kundin tsarin mulki | 8,250 | 11,750 | Ma'aikatar Lafiya<br>Karamar Hukumar Gaya | Kungiyoyi masu zaman kansu (NGOs)<br>LHC |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 8,250 | 11,750 | Karancin Ruwan sha | Karancin Ruwan sha<br>Hanyar samun ruwan sha (Tuƙa-tuƙa) | Haƙƙin Kayayyakin Aiki | Kundin tsarin mulki | 8,250 | 11,750 | Ma'aikatar Albarkatun Ruwa<br>Karamar Hukumar Gaya | H Kungiyoyi masu zaman kansu (NGOs) |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 8,250 | 11,750 | Hanya | Rashin ingantaccen Shugabanci<br>Rashin Wakilci nagari | Haƙƙin Kayayyakin Aiki | Kundin tsarin mulki | 8,250 | 11,750 | Ma'aikatar Ayyuka<br>Karamar Hukumar Gaya | Kungiyoyi masu zaman kansu. Masu taimakawa al'umma |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 8,250 | 11,750 | Wutar Lantarki | Rashin ingantaccen Shugabanci<br>Rashin Wakilci nagari | Haƙƙin Kayayyakin Aiki | Kundin tsarin mulki | 8,250 | 11,750 | Ma'aikatar Hasken Wutar Lantarki<br>Karamar Hukumar Gaya KEDCO | Hukumar Samar da Wutar Lantarki a ƙauyuka |

## KALUBALEN **DA KE FUSKANTAR GARIN GAMOJI A HALIN YANZU**

Gamoji ɗaya ne daga cikin garuruwa a ƙaramar humukar Gaya wandaa shekaru da dama ke fama da matsaloli masu ɗinbin yawa waɗanda suka haɗa da rashin ɗakin shan magani na zamani kuma na dundundun wanda zai iya ɗaukan ɗawainiyar lafiyar jama'ar garin. Haka kuma akwai buƙatar samar da ƙarin ajujuwa da malami a makarantu, ga rashin ingantaccen rowan sha, ga rashin ingantattun hanyoyi da matsalar rashin aikinyi ga matasa da rashin hasken wutar lantarki da sauran matsaloli.

An jera matsalolin wannan garin ta hanyar tsarin na matsalar da tafi ciwa al'umma tuwo a ƙwarya a sama.





Jama'ar wannan garin sun zabi matsalar mayar da ɗakin shan maganin garin zuwa na zamani tare da samar da kayayyakin aiki ta kasance matsala ta farko. Wannan shi zai rage matsalar mutuwar mata masu juna biyu yayin haihuwa da kuma haɓaka rayuwar mazauna yankin tare da raguwar asarar rayuka da sauran matsaloli. Haka kuma al'ummar wannan gari sun zaɓi matsalar ilimi a matsayin matsala ta biyu, inda suka buƙaci a samar musu da ƙarin ajujuwa da ƙwararrun malamai. Samar musu da waɗannan zai sa asami mutane masu ilimi a garin waɗanda zasu taimaka wajen haɓaka garin yadda zasu iya gogaiyya da sauran garuruwa maƙota a ƙaramar hukumar. Sannan kuma an zaɓi matsalar rashin aikin yi a matsala ta uku da ta fi ci musu tuwo a ƙwarya, saboda yadda matasa ke zaman banza wannan kuma shi zai iya jawo musu gurbacewar halayya a garin. Amma samar musu da sana'o'in dogaro da kai zai taimaka ya hana su cuɗanya da miyagun ɗabi'u.

## SASSAUKAR HANYAR JERA MATSALOLI

| AL'AMARI | MATA | YARA | MAZA | ADADI | MATSAYI |
|---|---|---|---|---|---|
| Lafiya: Haɓaka Ɗakin shan Maganin Garin | 18 | 119 | 150 | 287 | 1ST |
| Ilimi : Karin Ajujuwa da Malamai | 23 | 27 | 84 | 134 | 2ND |
| Rashin Aikin Yi | 23 | 08 | 74 | 105 | 3RD |
| Karancin Ingantaccen Ruwan sha | 16 | 07 | 25 | 118 | 7TH |
| Hanya | 12 | 07 | 12 | 31 | 8TH |
| Karancin Hasken Wutar Lantarki | 23 | 08 | 37 | 68 | 6TH |
| Kewaye Musu Maƙabarta | 14 | 06 | 50 | 70 | 5TH |
| Gyaran Masallacin Garin | 31 | 14 | 44 | 89 | 4TH |





Figure 12: Jama'ar Gamoji Yayin Jeran matsalolin



Figure 13: Kungiyoyin Mata Yayin Jeran matsalolin









## TANTANCE MATSALOLI TA AMFANI DA BISHIYAR MATSALOLI

Ita wannan bishiya na taimakawa wajen faiyace matsalolin al`umma da aka binchiko. Bishiyar matsalolin tana nuna dangantakar waɗannan matsaloli da dalilan afkuwarsu da kuma illar da suke da ita. Wannan bishiyar na nuna matsalolin da kuma bada damar sanya bakin duk wanda al`amarin ya shafa wajen gano dalilan afkuwarsu inda a karshe za`a magance su. Babbar matsalar ita ce rashin ɗakin shan magani na zamani kamar yadda tushen wannan bishiya ya nuna. Abubuwan da suka jawo matsalar da abubuwan da matsalar ta haifar an tattauna su da mutanen garin Gamoji kamar yadda bishiyar matsalolin da ke biye ta nuna.



KUNDIN SAMAR DA TSARIN CIGABAN GARIN GAMOJI 2016



# KUNGIYOYI/HUKUMOMI DA MASU IKO DA ZASU IYA TALLAFAWA GAMOJI



Abubuwan da suka biyo baya daga bishiyar matsaloli, an yi nazarin ƙungiyoyi da mutanen da za su iya bayar da gudummawa wajen warware matsaloli. Al'ummar garin Gamoji sun fitar da muhimman mutanen da suke da zarafin tallafawa domin samar da canjin da ake fata a garin.

| ABUBUWAN DA AKA GANO | WAƊANDA ZA SU IYA TALLAFAWA | CIBIYOYI | MANYAN BUKATU/ ZABURARWA DOMIN KAWO CANJI | MATAKIN KARFIN IKON KAWO CANJI ( SAMA TSAKA-TSAKI KO NA-KASA) |
|---|---|---|---|---|
| Karancin ɗakin Shan magani da ƙwararrun ma'aikatan lafiya. | 1.Dagaci<br>2.Kansila<br>3.Shugaban sashin kula da ɗakunan shan magani<br>4.Shugaban ƙaramar Hukumar Gaya<br>5.Kwamishinan Lafiya<br>6.Dan majalisar jiha<br>7.IliyasuGamoji<br>8.Abba Gamoji<br>9.ShehuGamoji<br>10.Dan majalisar Tarayya<br>11.Sanata | 1.Kwamitin ciyar da yankin gaba<br>2.Ma'aikatar lafiya<br>3.Ma'aikatar ƙananan Hukumomi<br>4.Majalisar Karamar Hukumar Gaya<br>5.Ma'aikatar Lafiya ta Tarayya. | 1.Cigaba<br>2.Siyasa<br>3.Cigaba<br>4.Siyasa<br>5. Siyasa<br>6. Siyasa<br>7. Siyasa<br>8. Siyasa<br>9. Siyasa<br>10. Siyasa<br>11. Siyasa | 1.M<br>2.M<br>3.M<br>4.H<br>5.H<br>6.M<br>7.L<br>8.M<br>9.L<br>10.M<br>11.M |
| Ilimi | Dai-dai da na sama | Dai-dai da na sama | Dai-dai da na sama | Dai-dai da na sama |
| Akwai buƙatar samarwa makaratar Sakandiren waje na dundundun da ƙarin ajujuwa da kuma malamai. Sai kuma ƙarin ajujuwa a Islamiyyar garin. | 1.Dagaci<br>2.Kansila<br>3.Shugaban sashin kula da ɗakunan shan magani<br>4.Shugaban Karamar Hukumar Gaya<br>5.Kwamishinan lafiya<br>6.Dan majalisar jiha<br>7.IliyasuGamoji<br>8.Abba Gamoji<br>9.ShehuGamoji<br>10.Dan Majalisar Tarayya<br>11.Sanata | 1.Kungiyar Iyayen Yara<br>2.SBMC<br>3.Tsaofaffin ɗalibai<br>4.Ma'aikatar Ilimi<br>5.Karamar Hukumar Gaya<br>6.Ma'aikatar Lafiya ta Tarayya | 1.Cigaba<br>2.Siyasa<br>3.Cigaba<br>4.Siyasa<br>5. Siyasa<br>6. Siyasa<br>7. Siyasa<br>8. Siyasa<br>9. Siyasa<br>10. Siyasa<br>11. Siyasa | 1.M<br>2.M<br>3.M<br>4.H<br>5.H<br>6.M<br>7.L<br>8.M<br>9.L<br>10.M<br>11.M |





## MUTANE

Bayan zayyana matsalar rashin ɗakin shan magani na zamani da ƙwararrun ma'aikatan lafiya a matsayin babbar matsalar dake damun al'ummar wannan gari, jama'ar garin sun tattauna akan wasu mutane da ƙungiyoyin da za su iya hubɓasa dangane da samar da ɗakin shan magani na zamani da ƙwararrun ma'aikatan lafiya saboda irin tasirin da suke da su na kawo chanji.

Al'ummar garin sun zayyana Gwamna da Shugaban Karamar Hukumar Gaya, da Kansila, Mambobin Majalisar Jihada Mabobin Majalisar Tarayya da Sanatoci, Kwamishinan Kananan Hukumomi Mai Unguwa/Dagaci Babban limami da mutanen da zasu iya kawo canji.

## KUNGIYOYI


Dangani da ƙungiyoyi kuma, an zayyana cewa Karamar Hukumar Gaya, Gwamnatin Jiha, Ma'aikatar Lafiya, Ma'aikatar Kananan Hukumomi, da Kwamatin Ayyuka na Majalisar Jiha, da masu ruwa da tsaki na da mutukar taka muhimmiyar rawa wajen kawo abubuwan more rayuwa a wannan gari.




## TANTANCE YANAYIN KARFIN IKO (NAZARI KAN WAƊANDA KEDA IKO)

An yi amfani da tsarin zane naVenn domin gudanar da wannan tantancewar. Haka kuma shi wannan ma`auni an yi amfani da tsarin zanen Venn domin tantance matakin da wutar lantarkin yake ko ikon da wani mutum ko wata ƙungiyoyi ke da shi da kuma alaƙarsu da juna.

Zanen dake tafe ya fitar da mutane da cibiyoyi waɗanda suke da ikon warware al'amari ko matsalar da aka gano.




Kwamitin ayyuka da gidaje na majalisar jiha nada mutaƙar tasiri da karfi wajen samar da canji dangani da haɓaka ɗakin shan maganin zuwa na zamani da kuma gyaran makarantu da samar da ƙarin ajujuwa da ƙwararrun malamai. Haka kuma yana da alaƙa da irin taimakon da Sanata da Wakilinsu na Majalisar Tarraya, Majalisar Karamar Hukuma da kuma al'ummar garin za su bayar. Ma'aikatar Ayyuka da Gidaje nada mutuƙar tasiri da kyakkyawar alaƙa da ma'aikatar ƙananan hukumomi da ƙaramar hukumar Gaya.Itama Majalisar Zartarwa ta ƙaramar hukuma nada irin wannan tasirin.Gashi kuma Majalisar Zartarwar Karamar Hukuma ita ce take sadar da buƙatun mutane da majalisar.
Rawar da masu sarautun gargajiya da yan kishin ƙasa ke da ita ƙalilan ce gurin samar da canji duk da cewa sun fi kusa da al'umma. Suma Malaman Addini da Kansiloli irin wannan rawar sukeda ita wajen kawo canji.







## TANTANCE MATSALOLIN DA KE ADDABAR GARIN GAMOJI

Tantance matsaloli hanya ce ta gano da auna da kuma jera matsalolin da ke fuskantar garindaki-daki. Bugu da ƙari, an gano Matsalolin da ke yiwa garin barazana. An yi amfani da jadawalin tantancewar wajen tattauna sabubban da suka haddasa su tare da tasirinsu.

### JADAWALIN TANTANCE MATSALOLI


| LAMBA | MATSALA | TASIRI | WAƊANDA SUKA FI CUTUWA |
|---|---|---|---|
| 1. | Zazzaɓin Maleriya | Mutuwa, Rashin Cigaban Al'umma | Gabaɗayan al'umma |
| 2. | Zaizayar Ƙasa | Mutuwa, Gurɓatar Yanayi | Gabaɗayan al'umma |



### TANTANCE HANYOYIN SAMUN BAYANAI

Garin Gamojina samaun bayanai daga waje ta hanyar gidajen radio da talabijin da zantukan jama`a da wayar tarho da masu shela, yanar-gizo, makarantu da sauran wajen tarukan addini a wannan yankin.Wasu lokutan waɗannan bayanai ana faɗarsu lokacin bukukuwan ɗaurin aure ko raɗin suna.

Amfani da wayar Salula da batutuwan al'umma hanyoyi ne da jama'ar wannan gari ke musayar bayani da jama'ar wasu garuruwan.Dagaci da masu sarautun gargajiya sune masu magana da yawun mutanen wannan garin.




## TSARIN DA AKA SHIRYA GUDANARWA NA AL`UMAR GARIN GAMOJI

A ƙarshen tattaunawar, an fitar da ƙwaƙƙwaran tsarin da za a bi domin warware matsalolin da aka gano ta hanyar samar da wani kwamiti wanda zasu haɗa ƙarfi da ƙarfe da CITAD domin magance abubuwan da ke ci wa al'ummar garin Gamoji tuwo a ƙwarya. Al`umar garin Gamoji sun binciko tare da gwada mizanin gazawar dake faruwa a yankin. An kuma yi amfani da wani teburin auna gazawa wajen tattauna waɗannan batutuwa.

Jadawalin da ke biye tsari ne na ayyukan da za aiwatar domin ganin mafarkin garin ya zama gaskiya na ganin an haɓaka ɗakin shan maganin garin zuwa na zamani.





| MAHIMMAN BATUTUWA | AIKIN DA AKA TSARA GUDANARWA | WAƊANDA SUKA ƊAUKI NAUYI | KAYAN AIKIN DA AKE BUKATA | MATSALOLI | SHAIDAR SAMUN NASARA | TSAWON LOKACI |
|---|---|---|---|---|---|---|
| Rangadi don saduwa da sauran jama`a a Garin Gamoji | Ganawar Baka-da-Baka Kiran Waya da Ganawa Samar da kwamiti | Yan Kwamitin Daftarin Cigaban Garin Gamoji<br>1. Zahara'u Madaki<br>2. Bashir Abdullahi-Chairman<br>3. ShehuTukur<br>4. Binta Yarmata<br>5. Gama Abdullahi<br>6.Isyaku Abdulkadir<br>7.Muhammad Ali<br>8.Hashimu Usman<br>9.Magaji S. Bello<br>10.Murtala Gentle | Bayani game da wannan shiri samar da Rukunin Al'umma | Zirga-zirga Kuɗin waya | Rahoto | 30 ga watan Oktoba Shekarar 2015 |
| Daftarin cigaban gari | Gabatarwa da amsar bayanai | CITAD/ Jami`in Gari | Albarkatun Dan`adam | Karancin Lokaci da Kayan Aiki | Kammalallen daftarin cigaban Gari | 30 ga watan Oktoba Shekarar 2015 |
| Kaddamar da Kundin Cigaban garin Gamoji | Raba wasiƙun gaiyata<br>-Haɗa gwiwa da kafafan yaɗa Labarai<br>-Tsara Taro | CITAD/ Jami`in Gari | Tuntuba Al'ummar Gari wasiƙu Sufuri Yaɗa saƙon a kafafen watsa labarai | Lokaci | Kaddamar da Kundin Cigaban Garin Gamoji | 30 ga Watan Nuwamba Shekarar 2015 |
| Ziyara domin samun mai gudanar da Aiki | Ziyarce-ziyarce | CITAD/ Jami`in Gari | Jama'ar gari littafin Kauye<br>-Kafar yaɗa Labarai | Lokaci | Sabgogi | Kwanan Watan Bayar da Rahoto |